
Babban Ofishin da]e Kula da Sha'anin Masallacin Haram da Masallacin Annabi, a Saudi Arabia

# SIFAR HAJJI DA UMRA

## TARA DA ZA|A||UN ADDU'OI



TARJAMAR

DR. AHMAD A. MAHMOUD

اللغة الهوساوية

*Jerin Wasi}un Shiryar da Alhazzai*
*Da Masu Yin Umra*
*Risalah Ta Huju*
*Bugu na biyar 1426 H*

**Jerin Wasi}un Shiryar da Alhazzai Da Masu Yin Umra**

**Risalah Ta Hu]u**

Babban Ofishin da}e Kula da
Sha'anin Masallacin Haram da Masallacin Annabi,
a Saudi Arabia.

# SIFAR HAJJI DA UMRA TARE DA ZA|A||UN ADDU'OI

Tarjamar
Dr. Ahmad A. Mahmoud

**Bugu na biyar 1422H**

www.gph.gov.sa

Farawa Da Sunnan Allah Mai Rahma, Mai Jin }ai

Allah Ma]aukaki yace:

(Kuma akwai hajjin [akin domin Allah a kan mutane, ga wanda ya sami ikon zuwa gare shi, kuma wanda ya kafirta, to, lalle Allah Mawadaci ne daga barin talikai) Al' Imrana Aya ta 97

Kuma Allah Ma]aukaki yace:

(Kuma ku cika hajji da umra domin Allah) Alba}ara, Aya ta 196



# Gabatarwa

Godiya ta tabbata ga Allah mai karamci mai yawar yin falala (ga bayinsa), yana bada falala ga wanda yaso daga bayinsa ta ni'imar imani, kuma ya shar'anta musu hajji zuwa ga [akinsa 'yantacce, kuma shi mawadaci ne akan dukkan talikai, ya cika mana addini, kuma da ni'imar sa akan mu, kuma yasa mu daga alummar da tafi alheri, muna umurni da a bunda aka sani (na shariah) da hani daga abin da ake }i.

Salatin Allah da Aminci sun tabbata a kan wanda aka aikosa don Rahama ga dukkan talikkai, wanda yake mafi alherin da ya ta~a yin aikin hajji da umra, wanda kuma ya bayyana muna da bayani mafi alheri hukunce-hukuncen ibadar Hajji, kuma yace: "Ku ]auki ibadar Hajjinku daga gareni", kuma ya umurce mu da yin aikin cikin kwanciyar hankali da girmamawa, saboda haka yace (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi): "Ya ku Mutane, Kuyi a hankali da natsuwa, domin shi addini bai kasancewa da gaggawa" watau da sauri da hanzari, domin kuwa, so dayawa haka nan yakan kaiga cutar da 'yan uwanka musulmai.

Lalle kawo zucciya kusa (ga Allah) and tsoransa akan samesu ne ta hanyar natsuwar ga~o~in jikin da tsanaki, domin shi abin da yake bayyane na zahiri shi kwatankwacin addreshin abin da yake ~oye ne, kuma lalle ne Annabi -(Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi)- ya ha]a tsakanin wa]annan abubuwan guda biyu a hajjin da yayi, saboda haka ya kasance mai zucciya falkakka wadda wani abun shagala bai ]auke hankalinsa ba daga ayyukan hajjinsa, kuma ya kasance mai tawadu'i da }as}antar da kansa zuwa ga Ubangijinsa Mareninsa, mai kuka da zubar ha hawaye, mai yawaita tadarru'i da }an}an da kai da yawan ganawa (da Ubangiji).

Kamar yadda ya kansance (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) mai }as}antar da ga~o~insa yana tafiya tafiya mai sau}i da natsuwa da tsanaki, yana aikata ayyukan hajji cikin halin mutunci da



www.gph.gov.sa

kwanciyar hankali. Jabir (Yarda Allah ta tabbbata agerishi) yace: "Manzon Allah (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) ya malalo daga (Arafat) yana cikin natsuwa da kwanciyar hankali." Saboda haka Umar bin Abdulaziz (Allah yamishi rahma) a locacin da yayi wa mutane hu]uba a Arafa, yace: "Wanda ya tsere wa mutane ba shine wandan ya tsere musu da ra}uminsa ba, amma wanda ya tseremusu shine wanda aka gafartatwa zunubbansa"

Soboda haka Ya kai mahajjaci da mai umra, kasa manzon Allah (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) ya zama abun koyinka da jagoranka, ka saka tufafin natsuwa da rigunan mutunci, kuma ka zo ka yi ayyukkan hajjinka da kwanciyar hankali da kula da ma'anar duk abinda kake cewa ko kake aikatawa, sa'annan kuma nisanci tsanantawa da shish-shigi a ibada domin mafi alherin alamunra shine tsakaitacce, kuma lalle yace (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi): "A kwai Hadaya madaidaiciya akan ku domin ba wanda zai tsananta akan addini face ya rinjayesa"

Lalle ne, Babban Ofishin da}e Kula da Sha'anin Masallacin Haram da Masallacin Annabi yana fata daga 'yan uwanmu Musulmai, a lokacin da yake bada wannan ]an littafin shiryarwa ga ayyukan hajji da umra mai kunshe da fa]akarwa ga wa]ansu kurakuran da alhajji ko mai umra yakan fa]a akan su, da su fahimci addininsu kuma suyi }o}arin yin aikin hajjinsu akan fuskar shariah kuma su gode wa Ubangijinsu mai girma da ]aukaka wanda ya sau}a}e musu yin hajji cikin sau}i da kwanciyar hankali.

Allah ya kar~i ayyukan mu na }warai da naku kuma ya bamu dacewa da abubuwan da yake so kuma ya yarda dasu. Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, kuma tsira ya tabbata ga annabinmu Muhammad da iyalansa da sahabbansa, da amincewa mai yawa.

Shugaban masu Kulla da Sha'anin Masallacin Haram da Masallacin Annabi.

***DR. Salih bin Abdullah bin Humaid***



# Bayanin farko na littafin

Godiya ta tabbata ga Allah, wanda ya saka hajjin ]akinsa tsararre ]aya daga cikin manyan ginshi}an addini, kuma ya bawa wanda yake so daga bayinsa muwafa}ar yin ]awafi a gidan da kuma yin sallah a bayan ma}ami Ibrahim ansawa ga kiran da Ibrahim al-khalil (aminci ya tabbata a gereshi) yayi kamar dai yadda Ubangijinmu (Mai girma da ]aukaka) ya umurcesa da cewa: "Kuma ka yi yekuwa ga mutane da wajabcin Hajji, su je maka suna masu tafiya da }afafu da kuma a kan kowane ma]ankwarin ra}umi masu zuwa daga kowane rango mai zurfi" sura ta hajj, aya ta 27.

Tsira da Amincin su tabbata ga mafi alherin mutane kuma shugaban manzanni, annabinmu da makoyinmu Muhammad bin Abdullah wanda aka aiko da addini mi}a}}e da Tsari madaidaici, wanda yace: "Ya ku Mutane, lalle ne Allah ya wajabta muku Hajji saboda haka kuje Hajji" Muslim ya ruwaitoshi.

Kuma lalle annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) ya shiryar da alummarsa zuwa ga yin Hajj ingantacce, saboda haka yace wa sahabansa (Allah ya yarda da su): "Ku ]auki ibadar Hajjinku daga gareni" Muslim ya ruwaitoshi. Saboda haka ya kwa]aitar da koyi da shiryarwarsa da kuma ri}e sunnarsa domin ibada bata zama ingantacciya sai ta kasance anyita musamman domin yardar Allah Ma]aukaki kuma mai dacewa da sunnarsa (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi).

Da ga wannan matashi, Babban Ofishin da}e Kula da Sha'anin Masallacin Haram da Masallacin Annabi yayi kwa]ayin rubuta wannan tunatarwa da lurarwa game da aikin Hajji da Umra domin ta haskaka hanyar ga masu zuwa [akin Allah Tsararre daga Alhazzai da masu umra domin suyi ibadodinsu akan fuska ingantacciya wadda ta dace da Littafin Allah da Sunna, kuma domin Musulmi ya kasance



www.gph.gov.sa

akan haske cikin addininsa domin ya nisanci duk abin da zai ~atamasa ibadarsa ko ya nakasata.

Kuma lalle ne a lokacin da muke gabatar da wannan }okarin wanda yake }aramine, muna ro}on Allah Mai Girma da [aukaka, yasa 'yan uwanmu Musulmi da su anfana da wa]annan shawarwari da fuskantarwa, kuma yayi muna da su kyautar fahimtar addini da yin ihilasi cikin magana da aiki, kuma ya kar~i ayyukanmu na kwarai dukkanmu, lalle ya kasance abin dogara da Mataimaki na }warai. kuma tsira ta tabbata ga annabinmu Muhammad da iyalansa da sahabbansa, da sallama mai yawa.



# Falalal Hajji da Umra

Hajji da Umra suna daga cikin ayyuka mafi falala wa]anda suke kankare zunubai da kurakurai, kuma masu kusantarwa zuwa yaddar Allah Ma]aukaki da aljannarsa. Domin kuwa duk wanda yayi hajji kuma baiyi jima'i ba da fasi}anci, zai koma kamar ranar da uwarsa ta haifesa (na rashin zunubai). Haka nan kuma Hajjin da yake kar~a~~e baida sakamako face Aljannah. Lalle ne an tambayi Annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) game da aiki wanda yafi duka (ayyuka) falala, sai yace: (Imani da Allah da Manzonsa), sai kuma akace: (Sai kuma wane?) yace: (sai kuma Jihadi cikin hanyar Allah) sai kuma akace: (Sai kuma wane?) yace:(sai Hajji kar~a~~e) Buhari da Muslim sun ruwaitoshi.

Kuma annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) yace: (Umra zuwa wata Umra, tana kankare zunubban dake tsakin su, kuma Hajji wanda yake kar~a~~e baida sakamako face Aljannah ) Muslim ya ruwaitoshi.

Kuma annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) yace (Wata Umrace cikin ramadan tana daidai da yin hajji tare dani) Buhari da Muslim sun ruwaitoshi.

www.gph.gov.sa

Kuma Aishatu (Allah ya yarda da ita) tace: "Ya manzon Allah, muna ganin cewa Jihadi shine mafi falalan ayyuka, shin baza muyi jihadiba? Yace: A'a, Jihadin da yafi falala (ga mata) shine Hajji kar~a~~e" Buhari ya ruwaitoshi.

Wannan babbar falalace da lada mai yawa wadda Allah majibinci yake baiwa bayinsa mumunai masu zuwa wa]annan kasace na tsarkakewa, da wuraren ibda na girmamawa, yana wa Mala'iku gori dasu a filin Arafat, yana ce musu: "Ku duba zuwa ga bayina, sun zo mun da yamutsentsen kai da }ura, Ina sheda muku cewa lalle na gafartamusu, " - "Babu wata rana da Allah yafi 'yanta bawa daga wuta a cikinsa fiye da ranar Arafa" Muslim ya ruwaitoshi.

Saboda haka ya chanchanta ga Musulmi daya gitta kansa ga kyaututtukan Allah kuma ya yi ganimar lokutan falala domin yaci nasara ta yardar Allah da Aljannarsa, kuma ya tsira daga hushin Allah da Wutarsa, domin shi Allah Ma]aukaki, mai yawan kyautane, me karamci, babu me halaka dominsa face halakakke da sha}iyi.



# Mi}atai

Kafin mu fara bayani game da sifar Hajji da Umra, zamu ambaci Mi}atan da ya wajaba a ]auki ihrami daga garesu ga wanda yayi nufin yin Hajji ko Umra. Wa]annan Mi}atan sun kasu kashi biyu: Mi}atai na zamani, da Mi}atai na wurare.

**Na farko**: Mi}atai na zamani, Ma]aukakai yace: (Hajjin watanni ne sanannu) Sura ta Ba}arah Aya ta 198. Watannin Hajji ko, sune Shawwal, da zul-}i'dah, da Goma na farko na zul Hijjah. Amma ita Umra ba tada wani zamani ke~antacce, ana iya yinta a ko wane lokaci a cikin shekara.

**Na Biyu**: Mi}atai na wurare: Sunna tasa iyakoki wa]anda bai halatta ga wanda yake nufin yin Hajji ko Umra da ya tsallakesu ko ya wucesu, in yabi ta hanyar su, face ya shiga cikin ihrami. Wa]annan Wuraren ko su biyar ne:

1. **Zul-Hulaifah:** Ana kiran wannan mi}ati a yau, Abar Ali, kuma shine Mi}atin mutanen Madina da wanda ya wuce ta madinah daga wa]ansunsu, kuma nisan wurin daga Makkah yayi kusa da kilomita 420.



www.gph.gov.sa

2. **Juhfah**: Ita wata al}aryace kusa da Rabig, kuma ita ce mi}atin mutanen Sham (Siriya) da Misira da Morroco da wa]anda suka wuce ta wurinta daga wa]ansunsu. kuma nisan wurin daga Makkah yayi kusa da kilomita 186. A yau, mutane sunna yin ihrami daga Rabig.

3. **{ar manazil:** Ana kiran wurin da sunan *Assail Alkabir*, kuma shi ne Mi}atin mutanen Najd da Ta'if, da wa]anda suka wuce ta wurinsa daga wa]ansunsu. kuma nisan wurin daga Makkah ya kai kilomita 78 a ta}aice, Kuma yana fuskantan wurinda akecewa **wadi Muhrim,** wanda yake sama ga **}ar manazil** ta fuskan hanyar Alhuda zuwa ta'if, kuma nisan shi daga Makkah Kilomita 75 ne a ta}aice.

4. **Yalamlam:** Shine mi}atin mutanen yamen da wa]anda suka wuce ta wurinsa daga wa]ansunsu, kuma nisan wurin daga Makkah kusa da kilomita 120 ne.

5. **Zatu-'r}in:** Ana kiran wurin da sunan *Addarbiya,* kuma shine mi}atin mutanen Ira} da wa]anda suka wuce ta wurinsa daga wa]ansunsu, kuma nisan wurin daga Makkah kusa da kilomita 100 ne.



Sa'anan wanda gidansa ya kasance bayan an wuce wa]annan mi}atan, zai ]auki ihraminsa ne daga gidansa. Amma wanda gidansa a garin Makkah yake, zai fita zuwa *hilli* (Wajen hurumin Makkah) don ]aukan ihramin umra, amma Hajji, mutanen Makkah sukan ]auki ihrami daga gidajensu da wurin zamansu.

**Fa]akalwa:**

Wanda ya biyo ta hanyar jirgin sama yana nufin Hajji ko Umra, ya wajaba akansa ya ]auki ihraminsa alokacin da yayi kunnen doki da daya daga cikin Mi}atai, kuma bai halatta ya jinkirta ihraminsa har sai ya sauka filin jirgi a Jeddah, domin Jeddah ba Mi}ati face ga mutanenta.

*(Wannan hukunchi bazai shafi Mahajjatan dake zuwa daga Yamma da Jeddah ba, domin basu }etare wani mi}ati ingantacce ta jihar da suka fito har su sauka a Jeddah, saboda haka alhaji zai iya ]aukan ihrahimsa daga Jeddah ko kan hanya idan ya daidaitu da mi}atin Juhfa wanda yake yafi kilomita ١٥ gabas daga ga~ar teku (da yawa a kan yi kuskuren kwatanta Jeddah da garin 'Rabig' wanda yake a bakin ga~ar tekun, alhali kuwa shima garin ba miqati ba ne na asali, lalurar ambaliyar ruwa da ta ci garin juhfa yasa mutane suke yin ihrami daga 'Rabig' kafin su iso Juhfa ), a ta}aice*



www.gph.gov.sa

*dai hukuncin Jeddah kamar dai garin Juhfa ne koko wanda ya isa garin Ta'if daga jihar Gabas, babu wani mi}ati ingantacce daga Ta'if harzuwa Makkah, saboda haka zai iya ]aukan ihrahimsa daga Ta'if ko kan hanya idan ya daidaitu da mi}atin }ar-manazil. - Ahmad)*

Idan kuma ya kasance babu tufafin ihrami tare dashi, sai ya cire rigarsa ya rufe kafa]unsa da }irginsa da ita, amma ya bar wandosa yayi niyyar yin ihrami. A lokacin da ya sauka a filin jirgin sama, sai ya saka tufafin ihrami kuma ya cire wandonsa, amma ita mace ba tada tufafin ihrami ke~antattu da ita, saboda haka sai ta ]auki ihraminta a cikin jirgin sama da tufafinta. Kuma idan ya kasance tasa *Bur}a* ko *Ni}abi* ([inkuna da Abubuwan rufe fuska) ko safar hannu, sai ta ciresu amma ta dinga rufe fuskarta da Gele a wurin mazaje baki (sune wa]anda shariah ta hana su kalleta).



# Ire'iren Ayyukan Hajji

Ire'iren ayyukan hajji guda uku ne. Ifradi, Tamattu'i, da }irani.

1. **Ifradi:**

Sifarsa itace alhaji zai ]auki ihramin yin aikin hajji kawai daga mi}atinsa, sai yace: *Labbaika Hajjan* (ina mai ansa kiranka na hajji). Idan ya isa Makkah sai yayi ]awafin }udumi (]awafin insowa), sa'anan sai yayi Sa'ayi tsakanin Safa da Marwa, bayan haka, bazai yi aski ko suisuye ba, kuma ba zai warware ihraminsa ba, zai tsaya cikinsa har sai yayi jifar *a}abah* a ranar idi, sa'anan yayi aski ko suisuye. Amma idan ya jinkirta yin Sa'ayi har zuwa bayan ya }are yin ]awafin Hajji (ifada), ya halatta a garesa.

2. **Tamattu'i:**

Sifarsa itace alhaji zai ]auki ihramin yin umra kawai amma ya kasance a cikin watannin hajji, sai yace: *labbaika Umratan* (ina mai ansa kiranka na umra). Idan ya isa Makkah sai yayi ]awafi da sa'ayi, sa'anan yayi aski ko suisuye. Bayan haka kome ya halatta a gare sa, sai kuma ranar takwas ga watan zul-hijjah wanda ake



www.gph.gov.sa

kira ranar *tarwiyah* sai ya ]auki wani ihrami don yin aikin hajji kuma ya zo da dukkan ayyukan hajji. Wanda yayi tammattu'i ya wajaba akansa ya yanka *Hadaya* a ranar yanka ko kwanakin zaman Mina guda uku. Wanda kuma bai samu yin yanka ba, sai yayi azumi kwana goma, kwanaki uku a lokacin aikin hajji, da bakwai bayan ya koma wurin iyalinsa.

**3. {irani:**

Sifarsa itace, alhaji yayi ihramin yin umra tare da hajji gaba ]aya sai yace: *Labbaika umratan wa hajjan* (ina mai ansa kiranka na umra da hajji) ko kuma alhajin zai yi ihramin yin umra daga farko sai kuma ya shigar da hajji kafin ya fara yin ]awafin umra. Soran ayyukan mai }irani kamar mai yin ifradi ne face ya wajaba akan mai }irani da ya yanka hadaya amma shi mai ifrad babu hadaya wajiba akansa.



# Rukunnan Hajji

Hajji yana da rukunnai guda hu]u, sune:

1. Ihrami, shine niyar shiga ayyukan hajji.
2. Tsayuwa a Arafa.
3. [awafin ifadah.
4. Sa'ayi tsakanin Safa da Marwa.

# Wajiban Hajji

Guda bakwai ne:

1. [aukan ihrami da mi}ati.
2. Tsayuwa a Arafat har fa]uwar rana.
3. Kwana a Muzdalifa.
4. Kwana a Mina kwanakin layya.
5. Jifan shai]an.
6. Aski ko suisuye.
7. [awafin wada'i (a mazhabar Malikiyah ba wajibi bane).

www.gph.gov.sa

**Fa]akalwa:**
Duk wanda yabar wani rukuni na hajji, hajjinsa bai cika sai ya kawo sa. Amma wanda yabar wani wajibi, *fidiya* ta wajaba akan sa, kuma zai yankata ne a Makkah, ya rarrabawa miskinan harami ba zai ci kome daga gareta ba.

## Rukunnan Umra

Guda uku ne:

1. Ihrami, shine niyar shiga umra.
2. [awafi.
3. Sa'ayi tsakanin Safa da Marwa

## Wajiban Umra

Umra tana da wajibai biyu:

1. Yin ihrami da mi}ati.
2. Aski ko suisuye.



## Abubuwan Da Aka Hana Yinsu A Cikin Halin Ihrami

Abubuwan da aka hana yinsu a cikin halin ihrami sun kasu kashi uku:

**Kashi na farko:** Abin da ya haramta akan Maza da mata.
**Kashi na Biyu:** Abin da ya haramta akan Maza banda Mata.
**Kashi na uku:** Abin da ya haramta akan Mata banda Maza.

**Na farko: Abin da ya haramta akan Maza da mata.**

1. Bayan niyar ihrami, baya halatta ga mai ihrami da ya cire wani abu daga gashinsa ko }unbarsa, amma in wani abu wa fa]i ba da gangan ba, babu kome akansa na fidiya (yanka).
2. Nisantar kowane nau'in Turare daga jikinsa ko tufan ihraminsa ko abincinsa ko abun shansa.
3. Baya halatta yasa safar hannu.
4. Mai ihrami bai halatta ya nemi aure ko ya ]aurawa kansa aure ko waninsa.
5. Jima'i ko mu}addimarsa basu halatta ga mai ihrami.



www.gph.gov.sa

6. Baya halatta ga mai ihrami da yayi farauta da kasheta ko korata ko taimakon wani a yinta. Amma yin farauta a cikin hurumin Makkah, baya halatta ga mai ihrami da wanda bai cikin ihrami.

**Na Biyu: Abin da ya haramta akan Maza kawai.**

1. Duk abin da aka ]inkashi kamar riga da wando da safa da makamancinsu baya halatta ga mai ihrami yasa su, sai dai in bai samu *izari* (abun ]aurawa kaman zane) sai ya sa wando, haka nan in bai samu *silipas* (takalma bu]a]]u kamar faje) zai iya sa takalmin huffi (takalma rufaffu).
2. Baya halatta rufe kai da wani abu da zai ta~ashi kamar hulla ko Rawani.

**Na Uku: Abin da ya haramta akan Mata kawai.**

Baya halatta ga mace da ta rufe fuskarta da Bur}a ko Ni}abi ko makamancinsu, amma yana wajaba akanta da ta suturta fuskarta ko ta kare da gele ko makamancinsa a cikin mazaje ba}i.



## Hukuncin wanda ya aikata wani abu daga cikin wa]annan abubuwan da aka hana.

1. Idan mai ihrami ya aikata abubuwan da aka hana domin <u>jahilci</u> ko mantuwa ko an tilastasa, babu wani laifi akansa, kuma babu fidiya akansa. (Abin kula shine *<u>jahilci</u> ko mantuwa ba su chanja hukunce-hukunce, saboda haka, gyara aikin da abin da ya lazimta shine tabbataccen al'amari- Ahmad*)
2. Mai ihrami zai iya aikata abubuwan da aka hana domin wata bu}ata, amma akwai fidiya akansa.
3. Idan mai ihrami ya aikata abubuwan da aka hana bada wani uzuri ba ko bu}ata, yaza mai laifi kuma akwai fidiya akansa.



www.gph.gov.sa

# Mi}idarin Fidiya

**Da farko**: Idan mai ihrami ya cire gashi ko }unba (akaifa), ko yasa turare ko safar hannu, koko namiji yasa ]inkakken tufa ko ya rufe kansa ko kuwa mace ta rufe fuskarta da ni}abi koko suka ]ha]u ha]uwan sha'awa, ga kowane abu daga cikin wa]annan abubuwan akwai za~in yin abubuwa uku (don gyara hajjin).

I. Azumi na kwana uku a jere ko dabandaban.
II. Ciyar da miskinai shida, kowane acikinsu rabin sa'i na abinci kamar dabino ko shinkafa ko waninsu.
III. Yanka tunkiya ko rago wanda za a rabawa fa}iran Makkah.

**Na Biyu**: Wanda ya bar wani wajibi daga cikin wajiban hajji ko umra, kamar ihrami daga mi}ati ko jifan shai]an ko kwana a Muzdalifa da sauran wajiban, ya wajaba a kansa yin fidiya. Yana isarmishi duk abin da ake layya da shi na namijin rago ko tunkiya ko bunsuru ko akuya, ko kuma abin da yake maimakonsu kamar kashi ]aya bisa bakwai na ra}umi ko saniya. Ana rabawa fa}iran Makkah duka naman kuma shi wanda yayi laifin bai halatta yaci wani abu daga naman. (Ba kamar naman hadaya ba).



**Na Uku**: Wanda yayi jima'i kafin warware ihraminsa na farko, hajjisa ya ~aci amma sai ya cigabi dashi haka nan, kuma ya ramashi shekara mai zuwa, kuma ya wajaba akansa da ya yanka ra}umi ko abin da yayi daidai dashi kamar Saniya ko tunkiya bakwai. Amma wanda yayi jima'i bayan warware ihraminsa na farko, ya wajaba akansa da ya yanka tunkiya ko abin da yayi daidai da ita kamar kashi ]aya bisa bakwai na ra}umi ko saniya. In kuma bai samu haka ba sai yayi azumi na kwana goma.

**Na Hu]u**: Game da sakamakon farauta. Yana da halaye biyu:

1. Idan naman farautar ya kasance yana da kwatankwacinsa (misalinsa) daga dabbobin layya, mai ihramin yana da za~i tsakanin abubuwa uku.

I. Ko ya yanka irinsa sa'anan ya rabawa fa}irai da miskinai na Hurumin Makkah
II. Ko ya fitar da }imar wannan dabba ya sayi abinci wanda za'a rabawa miskinai, kowane miskini a bashi rabin sa'i na abincin
III. Ko yayi azumi na kwanaki na iyakan adadin yawan miskinan.



www.gph.gov.sa

2. Idan naman farautar ya kasance baida kwatankwacinsa daga dabbobin layya, kamar Fara, mai ihramin yana da za~i tsakanin abubuwa biyu.

IV. Sai ya duba }imar naman farautar da aka kashe ya fitar da abinda yayi daidai da }imarsa na abinci wanda zai rarrabashi tsakanin miskinai, kowane a cikinsu a bashi rabin sa'i.

V. Ko kuma yayi azumi maimakon ciyarwar (adadin miskinan), ga kowane miskini azumin kwana ]aya.

**Na Biyar**: Fidiyar wanda aka tsare daga yin hajji.

Wanda ma}iyi ko waninsa (kamar ciwo) ya tsareshi daga yin hajji bayan ya shiga ihrami kuma baiyi shara]i ba a lokacin ihraminsa, zai yanka hadaya kuma yayi aski ko suisuye domin fita daga ihramin. Yana walwale ihramin ne da yin yankan a wurin da aka tsareshi a cikin haram ne ko a wajen hurumin Makkah, kuma zai bawa fa}irai naman. In kuma bai iya win hadayar sai yayi azumin kwana goma sa'anan yayi aski ko suisuye don walwale ihramin.



# Sifar Ihrami domin yin Umra Da Hajji

## Sifar Ihrami

An shar'anta wa mai son yin hajji ko umra da yayi wa]ansu abubuwa kafin ya shiga cikin halin ihrami. Wa]annan abubuwan kuwa sune:

1. A lokacin da ka isa zuwa mi}ati, mustahabbi ne kayi wanka da tsabtace jikinka kuma da cire gashin hamatta da gashin gaba, kuma ka yanke }unbakka (akaifa) saboda kada ka bu}aci cire wani abu bayan ka shiga ihrami.
2. Sunna ce kasa turare a jikinka da duk abin da ya sau}a}a na turare amma kada kasa turare akan tufan ihrami.
3. Namiji yakansa tufan ihrami wanda yake kamar zannuwa biyune ya ]aura ]aya kuma ya yafa ]aya. Kuma anfi son su kasance farare masu tsabta. Ita kuma mace takansa kome takeso na tufa ba tare da fitar da }awa ba, kuma ta cire abin da yake rufe fuskanta daga Bur}a ko ni}abi shine abin da aka ]inka daidai da fuska, kuma ta cire safar

www.gph.gov.sa

hannu, sai tasa gele a fuskanta tana suturtashi daga mazaje baki.

4. Idan matar ta kasance cikin haila ko jinin haihuwa, ta kanyi wanka da tsabtace kanta kuma ta ]auki ihrami kamar sauran mata, kuma tayi duk abin da alhaji yakeyi banda ]awafi a ka'abah. In kuma umra takeyi sai ta tsaya cikin ihraminta har sai tayi tsarki sa'anan tayi wanka ta cika umratta.
5. Bayan ka }are wanka da tsabtace jikinka da saka tufafin ihrami, sai kayi niya da zucciyarka irin ibadar da kakeso.
6. An shar'antawa mai inyar shiga ihrami da ya fa]i abin da yayi niyarsa na aikin hajji ko umra. In niyarsa yin umra ce, sai yace: "labbaika umratan". In niyar ta yin hajji ce kawai, sai yace: "Labbaika hajjan". In kuma niyar ta yin tamattu'i da umra ce zuwa hajji, sai yace: "Labbaikal lahumma umratan". In kuma yayi niyar yin }irani ne sai yace: "Labbaikal lahumma umratan wa hajjan". In kuma niyarsa ta yiwa wanninsa ne alhali yariga yayi umra da hajji nakansa, sai yace: "Labbaika hajjan 'an fulanin" ko "labbaika umratan 'an fulanin". Sai ya ambaci sunan mutumin maimakon cewa fulan.



7. Idan kuma kaji tsoron wani abu da zai iya hanaka cika aikin hajjinka, zaka iya shar]antawa lokacin yin ihrahimka, sai kace: "In wani abu ya tsareni, sai wurin warware ihramina yakasance a wurin da ka tsareni" Idan wani abu ya same ka wanda ya hanaka cika aikinka sai ka fita daga ihraminka kuma ba kome akanka.
8. Sunna itace ka yawaita ambaton Allah Ma]aukaki da yin talbiya, kuma sifar talbiya kamar haka: "Labbaikal lahumma Labbaik, Labbaika la Sharika laka labbaik, Innal hamda wal ni'mata laka wal mulk, la Sharika lak" (Ina mai ansa kiranka ya Ubangijina Ina mai ansa kiranka, Ina mai ansa kiranka babu abokin tarayya gare ka, Ina mai ansa kiranka, Godiya ta tabbata a gare ka da ni'ima da Mulki, Ina mai ansa kiranka). An Shar'anta wa maza da su yi a bayyane, amma mata, bai halatta da su bayyana ta a wurin maza ba}i.



www.gph.gov.sa

## Sifar Umra

1. Idan ka kai ( ka isa da zuwa) Masallacin ka'aba, sunna ce ka fara shiga da }afar dama sa'anan kace: "Bismillahi was salatu was Salamu 'ala rasulillahi, allahum magfir li zunubi waf tah li abwaaba rahmatika" Akan ce wannan a kowane masallaci.
2. Zaka tsayar da yin talbiya lokacin da ka isa ka'aba, kuma sai ka fara yin ]awafi daga 'ba}in Dutse' (hajarul aswad), kana mai sumbuntarsa ko ka ta~ashi da damanka sai ka sumbumci hannun naka, wannan kamar dai yadda ya sau}a}a a gare ka ba tare da ture-ture da 'yan uwanka Musulmi ba. Idan kuma ka kasa ta~ashi da hannunka, sai ka yi nuni da hannun zuwa ga ba}in dutsen (hajarul aswad), kace: "Allahu Akbar", sa'anan kayi ]awafi }afa bakwai, a kowane zagayowan kana farawa daga ba}in dutsen kuma ka }are dashi. Ana son kayi sassaka a ]awafin uku na farko, watau shine tafiya mai gaggawa tare da kusantar da taki, amma soran hu]un sai ka yi tafiya kawai. Ana son kuma kasa mayafin ihramin yadda hannunka na dama da kafa]a zasu kasaŋce a



waje a dukkan zagayowan. Ana yin haka ne a ]awafin }udumi da ]awafin umra. Amma shi sassaka da fitar da hannun dama da kafa]a, maza kawai keyin haka nan banda mata. Ana son ka yawaita yin addu'a da ambaton Allah Ma]aukaki, da girmamasa da neman gafara daga dukkan zunubai. Shi ]awafi baida wata addu'a musamman don sa, zaka iyayin addu'a da duk abin da kakeso.
3. Sunna ce ka shafi *rukun yamani* da hannunka na dama ba tare da sumbantarsa ba, kuma kace: "bismillahi wal Lahu Akbar", kuma tsakanin rukunnan biyu sai kace: "Rabbana Aatina fid Dunya hasanatan wa fil Aakhirati hasanatan wa }ina 'azaban Naar'.
4. In ka }are ]awafin sai ka rufe kafa]anka na dama da mayafinka kayi salla bayan Ma}ami Ibrahim (Aminci ya tabbata a gare sa), raka'a biyu, amma idan ka kasa yin sallar a wurin zaka iya yinta a kowane wuri a cikin masallacin. Sunna ce ka karanta '}ul ya ayyu hal kafirun' a raka'a ta farko bayan fatiha, kuma ka karanta '}ul huwal lahu ahad' a raka'a ta biyu.
5. Bayan ka }are sallar, sunna ce ka je wurin

www.gph.gov.sa

bakin dutsen ka ta~asa da sumbunta, in akwai sarari, sa'anan kasha ruwan zamzam.

6. Bayan haka sai ka nufi dutsen Safa ka hausa kana me karanta aya:

(إنَّ الصَّفَا وَالْمَرْوَةَ مِن شَعَائِرِ اللَّهِ فَمَنْ حَجَّ الْبَيْتَ أَوِ اعْتَمَرَ فَلَا جُنَاحَ عَلَيْهِ أَن يَطَّوَّفَ بِهِمَا وَمَن تَطَوَّعَ خَيْرًا فَإِنَّ اللَّهَ شَاكِرٌ عَلِيمٌ)

"Inas Safa wal Marwata min Sha'aa'iril Lah" Surar Ba}ara Aya ta 158. Ma'anar:(Lalle ne Safa da Marwa suna daga wuraren ibadar Allah, to, wanda ya yi hajin [aki ko kuwa ya yi Umra, to, babu laifi a kansa ga ya yi ]awafi gare su, su biyu. Kuma wanda ya }ara yin wani aikin alheri, to, lalle ne Allah Mai godiya ne, Masani). Mustahabbi ne ka fuskanci al}iblah ka yi hamdalah da takbiri, sa'anan kace:

(لا إله إلا الله وحده لا شريك له. له الملك وله الحمد يحي و يميت وهو على كل شيء قدير. لا إله إلا الله وحده. أنجز وعده. ونصر عبده. وهزم الأحزاب وحده)

"La ilaha illallahu wahdahu la sharika lahu, lahul mulku wa lahul hamdu, yuhyi wa yumitu, wa huwa 'ala kulli shai'in }adir, La ilaha illallahu wahdahu, Anjaza wa'dahu, wa nasara abdahu, wa hazamal ahzaaba wahdahu" Ma'anar: (Babu wani



abun bawtawa da gaskiya sai Allah shi ka]ai, bai da abokin tarayya, Mulki nashi ne, Godiya tashi ce, yana rayarwa kuma yana matarwa, kuma shi mai iko ne akan kome. Babu wani abun bawtawa da gaskiya sai Allah shi ka]ai, ya cika alkawalinsa, ya taimaki bawansa, kuma ya rusa }ungiyoyin shi ka]ai). Ka maimaita wannan addu'a so uku, sa'anan kayi addu'a da duk abin da ya sau}a}a.

Sa'anan sai ka sauka (daga Safa) ka yi tafiya zuwa Marwa, a lokacin da ka isa koriyar alama sai kayi sauri cikin tafiyarka har zuwa alamar ta biyu, amma mace, ba a shar'anta mata yin wannan saurin ba, abin da aka shar'antamata shine yin tafiya a ]awafin dukkansa.

Sa'anan sai ka chigaba da tafiya har ka hau Marwa, kuma kayi irin abin da kayi akan Safa, sa'anan sai ka sauka kayi tafiya wurin da ake tafiya, kuma kayi sauri wurinda ake sauri har sai ka isa Safa, kana haka nan so bakwai. Watau tafiya daga Safa zuwa Marwa sa'ayi ]aya ke nan, kuma dawowa daga Marwa zuwa Safa shima Sa'ayi ne ]aya, saboda haka zaka fara sa'ayi a Safa kuma ka }are a Marwa.

7. Mustahabbi ne ka dinga yawaita ambaton Allah Ma]aukaki a cikin sa'ayin ka, da kuma du'ai da duk abin da ya sau}a}a,



www.gph.gov.sa

kuma ka kasance mai tsarki daga hadasi, amma da zaka yi sa'ayi ba tare da tsarki ba zai isammaka. Haka nan ma mace, inda haila ya zo mata ko jinin haihuwa bayan ]awafi, ya halatta a gareta da tayi sa'ayi, domin shi tsarki ba shara]i ba ne ga sa'ayi sai dai mustahabbi ne.

8. Idan ka }are sa'ayinka sai ka aske gashin kanka ko kayi suisuye, amma aski (}waryal molo) ta fi falala ga maza, saide in ya kasance hajji a kusa yake, amfison yin suisuye do min yin askin a cikin hajji. Yin Suisuye ko aski a ~angare ]aya bai isarwa sai an game kan duka. Amma ita mace, tana rage gashin ta daga kowane dam}i kwatankwacin kan yatsa, koko ta tara dukka gashinta a kamu ]aya sai ta yanke gwargwadon kan yatsa.

9. Idan ka aikata wancan, umrakka ta cika, kuma ko abin da aka hanaka lokacin ihrami ya halatta gare ka. Amma in kana daga wan]anda suka koro dabbarsu ta hadaya daga hilli (Wajen Hurumin Makkah), sai ka tsaya a cikin ihraminka bayan ]awafi da sa'ayi, baza ka yi aski ba ko suisuye har sai bayan Arafa domin ka warware hajjinka da umar a tare.



# Sifar Hajji

1. A ranar tarwiyah, watau ranar takwas ga watan zul hijja, ana son ka ]auki ihrami don yin hajji daga wurin zaman ka a Makkah. Amma in ka jinkirta ]aukan ihramin har ranar tara, ya isar maka, sai dai yin haka nan sa~anin sunna ce. Ana son kayi wanka in akwai halin yin haka nan, sa'anan ka shafa turare kuma kasaka tufafin ihrami. Sa'anan kayi niyar hajji, ka ce: "Labbaika hajjan, Labbaikal lahumma labbaik … har }arshe"
2. Sai ka fita zuwa Mina, kayi salloli biyar, watau azzahar da la'asar, da magariba da Isha'i, da safe. Dukkan su a lokacin su ba tare da yin jamin su ba. Amma salloli masu raka'a hu]u sai ya sallacesu a }asaru watau bibbiyu.
3. Idan rana ta fito ran tara ga watan zul hijjah, sai ka tafi Arafat. Sunnace in da akwai sarari ka sauka a wurinda ake kira Namirah (an gina masallacin Arafat a wurin) har zuwa zawali. Bayan zawali sai kayi jam'i da }asaru na sallar azzahar da la'asar da kiran salla ]aya kowace da i}amar ta.
4. Ka kuma tabbata ka shiga cikin iyakokin Arafat. Ita Arafat dukkan ta wurin tsayuwa ce



www.gph.gov.sa

face cikin wurin da ake kira 'Urunah. Ana son ka yawaita yin Addu'a da zikirin Allah da }an}an da kai zuwa ga Allah Ma]aukaki, kana mai fuskantar al}iblah da ]aga hannayenka sama da }askantar da kanka. In kuma ka karanta wani abu na }ur'ani, to, yana da kyau.

5. Idan Rana ta fa]i, sai ka bar Arafa zuwa Muzdalifa cikin sukuni da natsuwa, kuma ka ya waita yin talbiya, kuma ka nisanci cutar da 'yan uwanka Musulmai. Idan ka isa Muzdalifa, sai kayi jam'i da }asarun sallar Magariba da Isha'i da kira ]aya da i}ama biyu. Sa'anan ka tsaya a Muzdalifa har sallar Safiya, bayan haka sai ka tsaya a wurin da ake kira Almash'aril Haram (wurin masallacin Muzdalifa) kana mai fuskantar al-}iblah, kuma ka yawaita zikirin Allah Ma]aukaki, da addu'a, tare da ]aga hannayenka sama har zuwa gari ya waye sosai. Amma kowane wuri a Muzdalifa ka tsaya a wurinsa ya isamma. Kuma akwai rangwame ga masu rauni daga mata da yara da sauransu da su tafi Mina bayan rabin dare ya shu]a.

6. Sa'anan ka nufi Mina kafin fitowar rana, kana mai yin talbiya. Ana son ka ]auki 'yan duwatsu guda bakwai masu girman tsakkuwar jifa ko iri na manyan wake, ko mai kama dasu. Ana son kayi tafiya da sauri a lokacin da ka isa rafin da



www.gph.gov.sa

ake kira muhassir (tsakanin Muzdalifa da Mina) a kan hanyarka zuwa Mina don jifa.

7. Idan ka isa Mina, sai ka tafi wurin jifar shai]an babban, wanda yake 'a}abah. Zaka tsaya da yin talbiyah a lokacin da ka isa wurin, sai ka jefi shai]an din da duwatsu bakwai ]aya bayan ]aya, kana mai yin kabbara a lokacin jefa kowane dutsen. Kuma shara]ine ya kasance kowane dutsen ya fa]a cikin wurin jifar. Kuma mustahabbi ne in ya sau}a}a, kasa Ka'abah daga jihar hagunka kuma Mina daga ta daman ka a lokacin jifa.

8. Bayan jifa, sai ka yanka hadaya idan ya wajaba akanka, kuma ana son kaci daga hadayar kuma ka ciyar da fa}irai. Shi kuma lokacin yankan ya kan kai har fa]uwar rana ga ranar uku da kwanakin layya.

9. Bayan yankan ko soke hadayar, sai ka aske gashin kanka ko kayi suisuye, amma shi askin yafi falala. Amma mace, takan yanke gwargwadon kan yatsa daga kowane dam}in kitsonta.

10. Wancan jerin na ayyukan shine mafi falala, amma in an }addama wa]ansu daga cikinsu a kan wa]ansu, to, babu laifi.

11. Bayan Jifa da aski ko suisuye, kasaka kayanka kuma kome halali ne gare ka banda Jima'i.

Wannan halacci watau warware ihrami shine na farko. Ana son kasa turare bayan haka sai ka nufi Makkah.

12. Idan ka isa Makkah, Kayi ]awafin ifadah, wanda ake kira ]awafin ziyarah. Bayan haka sai kayi salla raka'a biyu ta ]awafi bayan ma}ami Ibrahim idan akwai sarayin haka nan ba tare da yin turanreniya da mutane ba. Amma in akwai gwamutsin mutane, zaka iya sallar a kowane wuri cikin masallacin. Bayan haka sai kayi sa'ayi tsakanin Safa da Marwa, haka amma in ka kasance tamattu'i ka ]awka. Ko kuma }irani ko ifradi ne ka ]awka amma ba kayi sa'ayi ba lokacin da kayi ]awafin }udumi. Ya halatta yin jinkirin ]awafin ifadah da Sa'ayi daga ranar yanka (Ranar idi)

13. Bayan ]awafin ifadah a ranar yanka, sai ka koma Mina ka kwana a cikin ta darerakun kwanakin jifa, watau, daren goma sha ]aya, da na sha biyu, da na sha uku. Amma idan kayi hanzarin tafiya bayan kwanan dare biyu, to, ya halatta gare ka haka nan.

14. Za ka yi jifan shai]an a wuraren uku a ranakun jifar bayan zawali, kana mai farawa da na farko watau }arami, wanda yake bin masallacin haifa na Mina. Sa'anan ka jefi na tsakkiya, sa'anan ka jefi na 'a}abah. Kowane jifan da duwatsu



bakwai ]aya bayan ]aya, kana mai yin kabbara lokacin da kake jefa kowane dutsen. Ka tabbata kuma cewa kowane dutsen ya fa]a a cikin ramen wurin da ake jifan. Kuma sunna ceyin addu'a mai tsawo mai yawa bayan jifar farko da ta biyu.

15. Yana halatta a gare ka gaggauta barin Mina bayan jifar shai]an a rana ta goma sha biyu bayan zawali, amma ka fita daga Mina kafin faduwar rana. In kuma kayi jinkiri har zuwa ranar goma sha uku, to, wannan yafi falala, amma sai kayi jifar bayan zawali.

16. A lokacin da kayi }udurin komawa garinka bayan ka }are ayyukan hajji, ya wajaba akanka kayi ]awafin ban kwana shima zagayowa bakwai, sa'anan kayi Salla bayan Ma}ami Ibrahim raka'a biyu. Amma wannan ]awafin ya fa]i a ha}}in mai haila da jinin bi}i, aboda haka za ta iya tafiya ba tare da yin ]awafin ba.

www.gph.gov.sa

## Shiryarwa ga Alhazai da masu umra

[an uwana Musulmi da 'yar Uwata Musulma, wannan wa]ansu shiryarwa ne masu muhimmanci wan]anda ya kamata kowane Alhaji da mai umra ya koye su kuma ya kula da su, yayi aiki da su domin ibadar sa ta kasance ingartacciya da ikon Allah Ma]aukaki:-

1. Kyautata niya ga Allah Ma]aukaki, da neman abun da yake wurinsa, da nisantar riya da son aji.
2. Tuba na gaske daga dukkan zunubai da kurakure, tare da }an}an da kai da mi}a wuya ga Allah Ma]aukaki.
3. Koyan addinin Allah Ma]aukaki da fahimtarsa, da koyan abin da ya wajaba akanka na aikin hajji da umra da tambayan duk abin da yayi maka wahalar ganewa.
4. Tsare harshenka da ga~o~inka daga dukkan abin da yake jawo hushin Allah Ma]aukaki.
5. Yawaita tuna Allah Ma]aukaki da ambatonsa, da talbiya da du'ai, da istigfari, da ayyukan kwarai, dominfa kana cikin wuri wanda ake ri~inya ladar ayyukan kwarai.



6. A lokacin da isa mi}ati, kana da za~in ]aukan ko wane irin ihrami (}irani ko tamattu'i ko ifradi). Yana haramta a gare ka ka }etare mi}ati ba tare da ]aukan ihrami ba idan kana nufin yin hajji ko umra.
7. Idan ta jirgin sama kazo ya wajaba a kanka ka ]auki ihrami lokacin da kayi daidai da mi}atinka.
8. Idan gidanka bayan a wuce mi}ati ne, sai ka ]auki ihramin ka daga wurinka ba sai ka je mi}atiba.
9. Idan kaji tsoron rashin iya ayyukan hajjin, zaka iya yin shara]i lokacin yin ihrahim ka da cewa: "In wani abu mai tsarewa ya tsare ni, to, wurin halatta ta shine wurin da ka tsare ni"
10. Yana halatta ga mai ihrami }ulle zanen ihramin sa da ]aure shi da zare da ]aura jikkar tsare ku]i, da sa zobe da agogo da tabarau da abun ji na kunne.
11. Yana halatta ga mai ihrami sa wando idan bai samu izari ba (tufan daurawa), haka nan zai iya sa rufaffun takalma idan bai samu silipas ba.
12. Yana halatta ga mace da tayi ihrami cikin duk tuffan da take so, amma kada ta sa kayan maza da na fitinah da nuna jiki da

www.gph.gov.sa

}awa.

13. Mace za ta iya saukar da gelenta akan fuskarta idan taji tsoron maza ba}i zasu iya ganinta.
14. Yana halatta ga mace ta saka safa mai kauri da marasa kauri lokacin ihramin ta, haka nan ma zata iya ciresu ba tare da ya shafi ihramin ta ba.
15. Mace da ta ]auki hajjin tamattu'i kuma sai tayi haila kafin ]awafin umra, sai kuma lokaci ya }ure mata ba tayi tsarki ba har hajj ya zo, za ta iya ]aukan ihramin hajj sai ta zama mai }irani.
16. Mai ihrami zai iya wanka da wanke kansa kuma ya sosashi idan ya bo}aci haka nan amma da hankali.
17. Yana halatta ga mai ihrami wanke tufan sa da yayi ihrami cikinsa da sake waninsa. (Bai halatta yin wanka ko wanki da sabulu mai }anshi- Ahmad)
18. Yana halatta ga mai ihrami da ya shiga }arkashin rufin mota ko lema ko hema ko iccenya, ko ya ]auki kayansa a akai in akwai bu}atan haka nan.
19. Ana iya yin ]awafi ta bayan zamzam da ma}ami a lokacin cikuwa. Shi masallacin dukkanshi wurin yin ]awafi ne.



20. Wanda yazo da rana, zai iya jinkirta yin ]awafi har sai cikin dare, ko sa~anin haka ma.
21. Wanda Shakka ta zo masa game da zagayowa nawa yayi a ]awafi ko sa'ayi, sai ya gina akan abin da ya tabbata. Saboda haka wanda yayi shakkan shin uku yayi ko hu]u? sai ya cigaba akan uku, haka nan sauran.
22. Yana halatta ga wanda ya gaji lokacin ]awafi ko sa'ayi da ya zauna ya huta sa'anan ya cika shi bayan ya huta a tafiye ko a tura sa kan kujera ko makamancin ta.
23. Abin da yafi shine ha]a sa'ayi da ]awafi, amma in ya jinkirtasa babu kome, kamar dai yayi ]awafi farkon yini sa'anan yayi sa'ayi }arsensa.
24. Abin da yafi ga Alhajin da ya kasa yanka hadaya shine yayi azumin kwana uku kafin ranar Arafa domin ya kasance baiyi azuma ba ranar, domin Annabi –tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya hana yin azumi ranar Arafa ga mahajjaci, kuma domin rashin azumi zai fi bashi }arfin zikiri da ibada.
25. Yana halatta yin azumin kwana uku da na kwana bakwai a jere ko daban daban.



www.gph.gov.sa

26. In mai tamattu'i ya }are umrassa, kome ya halatta a gare sa har da jima'i.
27. Alhaji yana ]aukan ihramin hajji ranar fita zuwa Mina daga wurin kwanansa, ba ya wajaba a kansa ]aukan ihrami daga cikin makkah, ko masallaci ko }asan indararo. Kuma babu wani ]awafin wada'i a kansa domin fita daga Mina ko Arafa.
28. Abin da yafi shine Alhaji ya fita zuwa Arafa daga Mina a ranar tara bayan fitowan rana.
29. Lokacin tsayuwan Arafa ya kan kai har fitowar alfijiri ranar idi (watau ranar goma ga watan zul hijja).
30. Alhaji ya kan yi sallar magariba da Isha'i bayan isa Muzdalifa ko cikin lokacin magariba ne ko na Isha'i.
31. Yana halatta a tsinci duwatsun jifan shai]an a kowane wuri kamar Muzdalifa da Mina da sauransu.
32. Yana halatta ga masu rauni daga mata da yara da makamantansu da su ]unguma zuwa Mina daga Muzdalifa bayan wucewar rabin dare.
33. Yana halatta ga mai kula da }aramin yaro wanda ba zai iya jifa ba da yayi masa maimakonsa. Haka nan ma yarinya }arama,



sai waliyin ta yayi mata jifan.
34. Yana halatta ga wanda ya kasa jifa don ciwo ko tsufa ko ciki, da ya wakkala wani yayi masa maimakonsa.
35. Yana halatta ga wanda ya wakilci wani a jifa da yayiwa kansa jifan sa'anan yayi wa wanda ya wakilta a ko wace majefar uku. Ba wajibi ne ba akansa sai ya }are dukkan jifan na kansa sa'anan yayiwa wani, zai iya in ya }are nasa a kowane majefa da yayiwa wani.
36. Yana halatta ga wanda jifa ya wucesa da rana yayi shi da daddare, wanda kuma jifan yini ya wucesa zai iya ramashi a wanshekare bayan zawali sa'anan yayi jifan ranar.
37. Yana halatta a jefi shai]an daga kowace jihar a wurin jifar, da shara]in cewa dutsen ya fa]a cikin wurin jifar. Ba kuma shara]i ba ne sai ya tsaya a cikin wurin matu}an ya fa]an cikin wurin ko da ya fita waje ya isam misa.
38. Jera ayyukan ranar idi kamar yadda yake tafe, shi ne sunna: jifan 'a}abah, sa'anan yanka hadaya in ta zama wajibi, sa'anan aski ko suisuye amma aski yafi falala, sa'anan ]awafin ifadah. Yana halatta

}addama wa]ansu ayyukan daga cikinsu akan wa]ansu.

39. Yana halatta a jinkirtar da ]awafin ifadah da sa'ayi bayan ranar idi, amma mafi falala shine kada a jinkirtasu har bayan watan zul hijja.

40. Lokacin yanka ya kan kai har fa]uwar ranar a ranar goma sha uku, shine kwana na uku na kwanakin jifa, saboda haka kwanakin yanka sun kasance kwana hu]u, ranar yanka da kwana uku bayan sa.

41. Yana halatta ga mai ihrami da yayiwa wani aski ko suisuye ko da yana cikin ihrami da kansa.

42. Yana halatta ga mai ihrami da yayi aski ko suisuye a kowane wurin wanda yake so domin aski baida wuri musamman.

43. [awafin wada' (na ban kwana) yana fa]urwa akan mai haila da jinin bi}i.

44. [awafin ifadah ya kan isarma matafiyi maimakon ]awafin bankwana idan yayi niyar haka nan.

45. Yana halatta ga wanda yayi ]awafin bankwana ya sayi abin da yake bu}ata matu}ar ya kasance cikin zamani ta}aitacce, amma in ya ja lokaci sai ya sake yin ]awafin.



# Fa]akarwa akan wa]ansu kurakurai

Wa]annan fa]akarwa a kan kurakuren da wa]ansu Alhazzai da masu umra suke yi, ya wajaba a kan Musulmi da ya kula da su kuma yayi kwa]ayin ibadarsa ta kasance ingantacciya, kuma ya guji dukkan abin da zai ~atata ko ya nakasa ta.

Amma kafin ambaton wa]annan kurakurai wa]anda suka shafi aikin hajji da umra, ya zama wajibi a fa]akar akan al'amari mai mahimmanci wanda ya ha]u da asalin addini da tushensa, kuma al'amarin shine watau, wa]ansu Alhazzai da masu umra –Allah ya shiryar dasu-suna tafiya zuwa }abururuka a Makkah da Madinah suna masu neman isarwa (wurin Allah) da matattu kuma suna neman albarka da }abururuwansu da abin da yayi kama da wannan da ga ayyukan shirki da Allah ko bidi'oi wa]anda suka sa~awa a}idar Musulmai ta kwarai. Kuma ba su lazimtar ziyara ta shariah wadda take da lularwa da tunatarwa da lahira da yin addu'a ga mamata da nemammusu gafara bayan yimusu sallama. Lalle ne, Annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) yace: "Na kasance na hanaku ziyarar }abururuka, to ku sanifa, ku ziyarcesu, domin suna tunatar da mutuwa" Muslim ya ruwaitoshi.

Ziyarar }abururuka abune wanda aka shar'anta shi amma ba tare da tafiya wani gari ko doguwar tafiya

www.gph.gov.sa

dominsa ba. Kuma ziyara ce ke~antacciya da maza banda mata. Lalle ne ya kasance daga shiryarwarsa (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) idan ya ziyarci }abururuka, yimusu addu'a da neman musu gafara da rahmah bayan yin sallama a kan su.

Haka nan kuma daga cikin kurakuren akwai alhazzan da suke wahalar da kansu da ~ata lokutansu da dukiyarsu wurin tafiya wurare a Makkah da Madinah wa]anda basu da wata ala}a da aikin hajji ko umra ko wata ibadah. A Makkah sukan je kogon Hira' da kogon thawr da wa]ansunsu. A Madinah sun tafi masallatai bakwai, da masallacin al}ibilah biyu da masallacin algamama da wa]ansu wurare sanannu domin yin sallah da addu'a a wurin su. Duk wannan daga bidi'a ne domin babu wurare da masallatai a duniya wa]anda ake wa shirin tafiya kuma a yi niyar sallah a cikinsu face masallacin Makkah, da masallacin Annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi), da masallacin al'a}sa, da masallacin }uba' ga wanda yake cikin Madinah, bayan wa]annan babu wani dalili a kan falalassu na sallah akan sauransu.

Amma kurakuren da suka shafi ayyukan hajji da Umra sune:



## Na Farko: Kurakure Game Da Ihrami

1. Wuce mi}ati ba tare da ]aukan ihrami ba, saboda haka wanda ya wuce shi da niyar yin hajji ko umra ba tare da ]aukan ihrami ba, ya wajaba a kan sa da ya koma mi}atin ya ]auko ihramin idan zai iya yin haka, ko ko sai ya yanka fidiya rago.
2. Wa]ansu Alhazzan da masu umra suna tsammanin cewa saka tufafin ihrami shine ihramin ]in. Amma sahihin magana shine, ihrami shine niya da zucciya domin shiga ayyukan hajji ko umra, shi kuma sa tufafin yana ciki daga shiryeshiryen ihrami ne da kuma alamassa da wajibensa.
3. Wa]ansu mata suna tsammanin cewa tufafin ihrami suna da wani launi na musamman kamar kore ko fari, amma wannan kuskurene. Ita mace ya halatta a gareta da ta ]auki ihrami a cikin kayanta wa]anda ta saba da su, kuma ta nisanci duk tufan da akwai }awa da mai kama da na maza.
4. Wa]ansu mata suna tsammanin cewa

www.gph.gov.sa

idan ta iso mi}ati cikin jinin haila ko bi}i, sai ta bar ]aukan ihrami da zaton ta ko da waliyinta cewa ba'a ]aukanshi sai da tsarki daga haila. Amma sahihin abu shine haila da jinin bi}i basa hana mace ]aukan ihrami, kuma wajibi ne akanta tayi kome kamar yadda Alhaji yakeyi na ayyukan hajji banda yin ]awafi wanda za ta jinkirtar dashi har sai ta yi tsarki sa'anan tayi wanka sai taje tayi ]awafin, kuma ba sai ta tafi masallacin tan'imi ko mi}ati ba, matu}an ta ]auki ihramin ta daga gare shi tun farko.

5. Wa]ansu mata suna ]aura wani abu kamar rawani ko }elle domin ya ]aga abin da ke rufe fuskar su daga ta~a ta. To wannan matsawa kai ne abin da babu dalili akansa. Babu laifi akan mace da gelenta ya ta~a fuskan ta a gaban mazaje ba}i a wurin ta ta fuskar Shariah.

6. Wa]ansu mazan suna kware hannun dama da kafa]ar dama idan sun saka tufafin ihrami, alhali kuwa an shar'anta haka nan ne lokacin yin ]awafin }udumi da umra, amma bayan



haka kafa]u ana rufe su da mayafi.

## Na Biyu: Kurakure Game Da [awafi

1. Wa]ansu ma]awafan su kan fara ]awafi kafin isa ba}in dutse (hajarul aswad), amma abin da yake wajibi shine farawa daga garesa. Ya kan fara da daidaita kafa]an sa na hagu da ba}in dutsen kuma ya }are a wurin.

2. Wa]ansu ma]awafan su kan lazamci wa]ansu addu'oi na musamman a lokacin ]awafi, wani lokacin ma ya kan karanta su da sauti a ]age kuma wasu jama'a suna maimaitawa bayan sa da sauti ]aya suna mai ru]awa wa]ansu a addu'ar su. Ita shariah bata zo da wata addu'a ke~antacciya don ]awafi ba face abin da ake cewa tsakanin rukunin yamani da ba}in dutse (hajarul aswad), watau:

( رَبَّنَا آتِنَا فِي الدُّنْيَا حَسَنَةً وَفِي الآخِرَةِ حَسَنَةً وَقِنَا عَذَابَ النَّارِ )

Ma'ana: "Ya Ubangijinmu! Ka ba mu mai kyau a cikin duniya da mai kyau a cikin lahira,



www.gph.gov.sa

kuma ka tsare mu daga azabar wuta"

3. [awafi baya inganta cikin hijri Ismail (wurin da a ka kewaye }arkashin indararon ka'abah tafuskar arewa) domin sashensa daga ka'abah ne, saboda haka wanda yayi ]awafi yabi ta cikinsa ba ya inganta kuma sai ya sake ]awafin.
4. Wa]ansu ma]awafan su kan yi sassaka a zagayen bakwai na ]awafi, alhali kuwa ba a yinsa sai a zagaye uku na farko, kuma a ]awafin }udumi kawai.
5. Wa]ansu ma]awafan su kan yi turereniya da cutar da wa]ansu wurin }o}arin sumbuntar Hajarul aswad (wanda wa]ansu ke cewa 'shan nono'). Wa]ansu har su kan kai ga zagi da dukan wa]ansu, saboda haka su }are ayyukansu da zunubi domin kuwa shi sumbuntar dutsen ba shara]i ne ba na ingancin ]awafi.
6. Wa]ansu ma]awafan su kan ta~a dukkan rukunen ka'abah, ko dukkan bangwayen ta kuma suyi ta shafan ma}ami Ibrahim, amma sunna itace ta~a Hajarul aswad da sumbuntar sa



ko nunashi da hannu, da kuma ta~a rukunin yamani.

7. Wa]ansu ma]awafan su kan yi turereniya domin yin sallah a wurin ma}ami Ibrahim, wannan ko yana }untatawa masu ]awafi alhali kuwa su raka'oin biyu za'a iya yinsu a ko'ina a cikin masallacin.
8. Wa]ansu matan sukan kutsa cikin mazaje domin ta~a Hajarul aswad, wannan baya halatta domin sharrin dake cikinsa da kuma fitnah.

## Na Uku: Kurakure Game Da Sa'ayi.

1. Wa]ansu masu sa'ayi suna ganin cewa sa'ayinsu baya cika sai sun hau har }arshen dutsen Safa ko Marwa har zuwa bango, amma abin da ya wadatar shine hawan dutsen kawai, kuma haka nan sa'ayin ya inganta.
2. Wa]ansu masu sa'ayi sukan zagayo har so goma sha hu]u su]are sa'ayin a Safa. Wannan kuskure ne. Wajibi

www.gph.gov.sa

shine zagayowa bakwai, daga Safa zuwa Marwa ]aya, kuma daga Marwa zuwa Safa ]aya saboda haka sai ya }are a Marwa.

3. Wa]ansunsu su kanyi sauri a cikin dukkan sa'ayin. Amma sunna itace yin sauri tsakanin alamoninnan kore guda biyu kawai, sa'anan ya cigaba da tafiya a sauran wuraren, kuma shi yin saurin maza kawai keyi banda Mata.
4. Wa]ansun su idan sun haw Safa da Marwa sukan fuskanci ka'abah sa'anan suyi kabbara da hannayensu kamar suna cikin sallah, to, wannan ishara kuskure ce. Sunna dai itace ]aga tafin hannu domin addu'a kawai, kuma ya gode Allah da yin takbiri yana fuskantar al}ibilah.
5. Wa]ansu masu sa'ayi idan sun }are sa'ayin sukan yi raka'a biyu kamar yadda akeyi bayan ]awafi, to, wannan bidi'a ce.
6. Wa]ansu masu sa'ayi su kan cigaba da yin sa'ayin bayan an tayar da Sallah da gurin ya }arasa zagayowan daya fara, to wannan ma kuskure ne domin wajibin da ke kanshi shine yin sallah



tare da mutane bayan haka sai ya cika zagayowan sa.

## Na Hu]u: Kurakure Game Da Arafa.

1. Wa]ansu Alhazzan ba su tabbatar da iyakokin filin Arafa, sai su sauka a wajen shi kuma su tsaya nan har fa]uwar rana sa'anan su tafi Muzdalifa ba tare da sun samu tsayuwan Arafa, wannan kuwa yana sa Hajjin ya ku~uce domin tsayuwan Arafa shine Hajjin.
2. Wa]ansu Alhazzan sukan bar Arafa kafin fa]uwar rana, wannan abune wanda bai halatta domin wajibi ne da su tsaya a Arafa har sai rana ta fa]i. Duk wanda ya fita daga Arafa kafin fa]uwar rana kuma bai komo ba akwai jini akansa.
3. Wa]ansu Alhazzan sukan yi turereniya domin hawan dutsen Arafa -wanda a ke kira Dutsen rahma- domin suyi sallah a samansa, to wannan jahilcine, domin shi Arafa dukkansa wurin tsayi ne kuma hawan

www.gph.gov.sa

dutsen bai zo cikin aikin hajji, haka kuma ke~esa da yin Sallah.

4. Wa]ansu Alhazzan sukan fuskanci dutsen Arafa da Addu'a, to, wannan ma kuskurene, domin wajibi shine fuskantar al}ibila.
5. Wa]ansu Alhazzan sukan tara tulin kasa da duwatsu ranar Arafa a wurare sanannu, wannan kuma aikin bidi'a ce wanda babu wani dalili akansa.
6. Wa]ansu Alhazzan sukan yi gaggawa lokacin tunku]ar mutane daga Arafa zuwa Muzdalifa, suna damun Musulmai kuma suna rigegeniya da motoci tare da danna hon ]in muta. To wannan ma kuskurene, domin sunna itace tafiya da tsanaki da hankali.

## Na Biyar: Kurakure Game Da Muzdalifa.

1. Wa]ansu Alhazzan sukan fara tara duwatsun jifa da isarsu Muzdalifa kafin suyi sallar Magariba da Isha'i, tsammaninsu cewa haka nan sunna ce, alhali kuwa sunna itace tsintar duwatsun bayan a bar Muzdalifa zuwa



Mina, kuma yana inganta da a tsincesu a ko'ina.

2. Wa]ansu Alhazzan sukan fita daga Muzdalifa kafin rabin dare kuma ba su kwana a cikin ta ko wanda ya bar kwana a Muzdalifa ba tare da uzuri ba lalle ne, ya bar wani wajibi daga wajiban Hajji.

## Na Shida: Kurakure Game Da Jifa.

1. Da ga cikin kurakuren da suka ha]u da Jifa, turenreniya da ya}i domin jifar shai]an, sa~anin abin da shariah ta zo dashi na yin abu a hankali da rashin cutar da Musulmai.
2. Wa]ansu Alhazzan sukan jefa dukkan duwatsun gaba ]aya maimakon jefa su ]a]]aya tare da yin takabiri a lokacin jefan.
3. Wa]ansu Alhazzan sukan yi imanin cewa lokacin da suke jifan Shai]an, cewa Shai]an ne (a gaske) suke jifa saboda haka sai su dinga yin yekuwa da ihu da zagezage da tada hankali da kai duka ga ginin wurin jifar da



www.gph.gov.sa

takalma da manyan duwatsu. To wannan jahilcine, domin shi jifar wurin ansa shine domin ambaton Allah Ma]aukaki, kuma dutsen ya kasance }arami kamar tsakkuwa yafi }wayar *himmis* girma da ka]an.

4. Wa]ansu Alhazzan sukan wakilta wa]ansu suyi musu jifa do min tsoron wahala da cunkoson mutane, amma ingantacciyar magana itace cewa wakilci baya halatta a aikin farilla sai tare da gazawa domin ciwo ko makamancinsa.

5. Wa]ansu Alhazzan sukan yi jifa ba'a cikin lokacin jifan ba. Kamar jifan 'a}abah kafin rabin dare ya wuce daren idi, ko yin jifa a kwanakin jifa uku kafin zawali. To wannan jifan ba ya wadatarwa domin an yisa ne ba a cikin lokacinsa ba, saboda haka sai ya sake sa. (*Wannan shine ra'ayin jamhurin malamai, amma saboda Mutuwar da akeyi wurin jifa kadai domin yawan Mutanen, yawan da bai kasance a da ba, yin rangwame akan bin mazhabobin wa]ansu tabi'ina da suka yarda a yi jifa bayan fitowar rana kafin zawali ya zama al'amarin kula dashi- Ahmad* )



6. Wa]ansu Alhazzan sukan yi jifa ba a tsarin yadda akeso ba, kamar su fara jifan daga wurin jifan shai]an na 'a}abah wanda daga garesa sai hanyan Makkah, maimakon farawa daga }aramin na farko wanda yake daga bayan masallacin haifa.

7. Wa]ansu Alhazzan ba su kula da kuma tabbatawa a lokacin jifa da ganin cewa dutsen ya fa]a cikin ramen majefar. Kuma dutsen kan iya dukan ginsi}in ba tare da ya fa]a cikin wurin jifar ba, saboda haka bai wadatarwa.

8. Wa]ansu Alhazzan sukan }addama jifar ranakun }arshe zuwa ranar jifar ta farko sa'anan ya tafi kafin ya cika hajjinsa. Ko kuma ya wakkala wani wandan zai masa jifan soran ranakun, shi kuma ya tafi garinsu. To wannan, wasa ne da wargi da ayyukan hajji, kuma ita gaggawa daga Shai]an ta ke. Domin jahilci sai Alhaji ya bar wajibai na aikin hajji masu yawa kamar jifa da kwana Mina ranakun jifar.



www.gph.gov.sa

## Na Bakwai: Kurakure Game Da Muna.

1. Wa]ansu Alhazzan sukan bar Mina zuwa Makkah a ranar }arshe ba tare da yin jifa ba sai suyi ]awafin bankwana sa'anan su dawo Mina suyi jifa daganan kuma sai su tafi garuruwansu. A haka zai kasance aikinsa na }arshe a hajji shine jifa ba ]awafin bankwana ba.
2. Daga cikin Alhazzan Wa]ansu sunyi mugunyar fahimta abin da a ke nufi da gaggawta tafiya bayan kwanaki biyu na ranakun jifa, sai suyi tsammanin cewa abin da a ke nufi shine ranar idi da mai bimishi, alhali kuwa abin da a ke nufi da kwanakin biyu sune bayan idi da kwana biyu, watau, ranar goma sha ]aya da sha biyu, wanda ya gaggawta a cikinsu da tafiya bayan zawali na ranar sha biyu bayan jifa, babu laifi akansa, kuma wanda ya jinkirta zuwa ranar goma sha uku bayan zawali babu laifi akansa, amma yafi falala.



## Na Takwas: Kurakure Game Da Fita Daga Masallacin Haram.

Wa]ansu Alhazzan idan suka }are ]awafin bankwana sai su fita da ga masallacin haram ta bayabaya, watau tafiya ta bayabaya ba tare da juyawa Ka'abah baya ba. Suna ganin haka shine daidai kuma ladibi ne. To wannan bidi'ah ce wadda aka }ir}iro. Allah shine mafi kowa sani.

www.gph.gov.sa

# Shiryarwa Ga mai ziyarar Masallacin Manzo

(Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi)

1. Sunna ce ziyarar Masallacin Manzon Allah (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi), a kowane lokaci, kafin hajji ko bayan hajji. Haka nan yin salla biyar cikinsa sunna ce. Ana son yawaita ambaton Allah da tunasa, da addu'a da sallar nafilah a cikinsa domin ita salla a cikinsa yafi alheri da yin salla dubu a cikin wanninsa face masallacin Makkah.
2. Sunna ce ga mai ziyarar Masallacin Annabi da ya fara da sallah raka'a biyu gaisuwa ga Masallacin. Yafi falala idan ta kasance a wurin da ake kira *Raudah* domin abin da ya zo na falalalta, amma kowane wuri ya sallace ta, zai samu falalar.
3. Bayan haka, sunna ce ya ziyarci }abirin Manzon Allah (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi) da yimasa sallama da sahabansa biyu, tare da ladabi da rashin ]aukaka sauti. Baya halatta ]aukaka sauti a wurin }abarinsa (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi) domin shi a girmamashi a halin rai da Mutuwa.
4. Sunna ce zuwa ziyarar masallacin }uba da yin salla a cikin sa domin falalar haka nan.
5. Sunna ce ziyarar ma}abartar Ba}i'i da }aburrukan shuhada'u na Uhudu da }aburrukan Sahabbai –Allah ya yarda da su- tare da yimusu addu'a, domin Annabi (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi) ya kasance yana ziyartarsu da yimusu addu'a.
6. Babu yin ihrami ko talbiya ko saka tufafi ke~antattu ko yin bankwana a cikin ziyarar Masallacin Annabi kamar yadda yake a masallacin Haram.
7. Baya halatta ga kowa da ya tambayi Manzon Allah (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi) ko wanninsa daga mamata ko wa]anda ba sa nan, biyan bukata ko kauda musiba ko warkewa daga wani ciwo daga abubuwan da babu mai iko akansu sai Allah Mai girma da Daraja, domin yin

www.gph.gov.sa

haka nan shirki ne dashi.

8. Ziyarar }abarin Manzon Allah (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi), da }abururukan Sahabbai da shuhada'u duk sunna biyene }ar}ashin ziyarar Masallacinsa (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi), domin tafiyar ibada ba ta kasancewa sai domin masallacinsa (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi).
9. Ita ziyarar Masallacin Annabi mai daraja, ba tada wani ala}a da aikin hajji, kuma ba cikin abubuwan da ke cika aikin ba ne. Ita ziyarar ba tada wani lokaci }ayyadadde a cikin shekara.
10. Babu wani adadi na sallolin da ya kamata mai ziyara ya yi su a masallacin.
11. Wanda ya keso yin Addu'a a cikin masallacinsa (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi), sai ya fuskanci al}ibla kuma baya halatta a gareshi da ya fuskanci ]akin manzo lokacin addu'ar.
12. Baya halatta da a shafa ]akin manzo ko a sumbuntasa ko ayi ]awafinsa



domin haka bidi'a ce wanda a ke }yama.

13. Sunna ita ce a lokacin ziyarar }abarinsa (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi), mai ziyarar ya tsaya a gabansa yana mai fuskantarsa sa'anan yace da ladabi ba tare da ]aukaka murya ba: (Assalamu 'Alaika Ayuhan Nabiyu wa Rahmatul lahi wa Barakatuh) Ma'ana: Amincin ya tabbata a gare ka ya kai Annabi, tare da rahamar Allah da albarkacinsa. Sa'anan yayi masa salati kuma yayi masa addu'a. In kuma mai ziyarar yace: "Amincin ya tabbata a gare ka ya Annabin Allah, Amincin ya tabbata a gare ka ya za~a~~en Allah daga Halittunsa, Amincin ya tabbata a gare ka ya shugaban manzanni da masu tsoron Allah, Ina shaida cewa ka isar da sa}o, kuma ka bayar da Amana, kuma kayi wa alummah nasiha, kuma kayi jihadi domin Allah iyakan jihadin" wa]annan dukkansu sifofinsa ne, babu laifi da cewa haka nan.

*(Saidai, daga cikin nasihar manzon Allah –*



www.gph.gov.sa

*Aminci ya tabbata agare sa- ga alummassa, shine hanawarsa garesu da kada su fifitashi akan sauran annabawa da kirari ko yabo-buhari ya ruwaito haka- Ahmad)*

Sa'anan sai yayi wa Abubakar da Umar (Allah ya yarda da su) sallama kuma yayi musu addu'a kuma ya nemammusu yardar Allah.

14. Bayan masallacin Annabi da masallacin }uba, babu wani masallaci a cikin madinah wanda shari'a tace a ziyarceshi, hunkuncin sauran masallatan dukka ]aya ne, babu wata falala akan su fiye da sauran masallatai.



# ZA|A||UN ADDU'OI

Ya Allah! Godiya ta tabbata a gare Ka mai yawa da kyau da albarka kamar yadda kakesu Ubangininmu kuma Ka yarda da ita. Godiya wadda bata yankewa ko ta ~aci ko ta lalace, cike da sammai da }asashenka, kuma cike da dukkan abin da Ka ga dama daga baya, da adadin abinda masu gode maka suka gode, kuma da adadin da masu gafala daga ambatonka suka gafala, Tsira da Amincin su tabbata akan bawanka da manzonka Muhammadu, }arshen annabawa da manzanni, kuma mafi alherin halittunka, kuma amininka a kan wahayinka, da kuma alayensa da sahabansa gaba ]aya.

Ya Allah! Godiya ta tabbata a gare Ka, Kai ne hasken sammai da }asa da abin da ke cikin su, kuma Godiya ta tabbata a gare Ka, Kai ne mai kula da sammai da }asa da abin da ke cikinsu, kuma Godiya ta tabbata a gare Ka Kai ne Gaskiya, kuma alkawalinka shine gaskiya, kuma maganarka ita ce gaskiya, kuma ha]uwa da Kai shine gaskiya, kuma aljanna gaskiya ce, kuma wuta gaskiya ce, kuma tashin }iyama gaskiya ne, kuna annabawa gaskiya ne, kuma Muhammad gaskiya ne.

Ya Allah! Kai ne na mi}awa wuya, kuma akanKa na dogara, kuma da Kai ne na yi imani, kuma zuwa wurinka na komo, kuma dominka na yi jayayya, kuma zuwa gare Ka nake neman hukunci, saboda haka Ka gafarta mun abin da ya gabata da ya jinkirta da na ~oye kuma na bayyane, Kai ne na Farko da na {arshe babu abun bautawa da gaskiya sai Kai, kuma babu karfi da iko sai tare da Allah ma ]aukaki mai girma.

Ya Allah! Kaba raina tsoronsa, kuma Ka tsarkakeshi, Kai ne mafi alherin da ze tsarkakeshi, Kai ne Waliyinsa da ubangijinsa.

Ya Allah! Ina neman tsari daga ilimi wanda bai anfanarwa, da zucciya bata jin tsoro da rai da be }oshi, da addu'ar da ba'a kar~a.

Ya Allah! lalle ina ro}onka domin Kai ne mai godiya babu wani abun bautawa sai Kai, wanda ya }ir}iro sammai da }asa, Ya mai ]aukaka da Girmamawa, Ya wanda yake rayayye, mai kulla da kume, ina son Ka gafarta mini kuma kayi mini rahama, kuma idan Ka nufi mutane da fitina, Ka ]auke raina zuwa gare Ka ba tare da Ka fitine ba.

Ya Allah! Ubangijinmu! Ka bamu abu mai kyau a cikin duniya da lahira kuma Ka karemu daga azabar wuta.



Ubangijinmu! Munyi imani saboda haka Ka gafarta muna, kuma kayi muna rahma, Kai ne mafi rahamar masu rahama.

Ubangijinmu! kada Ka karkatar da zukatanmu bayan Ka shiryardamu kuma kayi muna kyautar rahama daga gare Ka lalle ne Kai me yawan kyautane.

Ya Ubangijinmu! kada Ka kama mu in mun manta ko muka yi kuskure, Ya Ubangijinmu!kada Ka sa nauyi a kanmu kamar yadda Ka sa shi a kan wa]anda suke gabaninmu. Ya Ubangijinmu!kada Ka sanya mu ]aukar abinda babu iko gare mu da shi. Kuma Ka yafe daga garemu, kuma Ka gafarta mana, kuma Ka yi jin }ai gare mu. Kai ne Maji~incinmu, saboda haka Ka taimake mu a kan mutanen nan kafirai.

Ya Ubangijina! Ka sakani daga masu tsayar da sallah, haka nan ma daga zurriyata, Ya Ubangijinmu! Ka kar~i addu'armu, Ya Ubangijinmu! Ka gafarta mini da uwayena biyu da mumunai a ranar da za'ayi lissafi.

Ya Ubangijinmu! Ka ba mu sanyin idanu daga matanmu da zuriyarmu, kuma Ka sanya mu shugabanni ga masu ta}awa.

Ya Ubangijinmu! Ka ba mu wata rahama daga gare Ka, kuma Ka sau}a}e mana (samun) shiriya daga al'amarinmu.

Ya Ubangijinmu! kuma Ka bamu abin da Ka yi mana alkawari a kan manzanninka, kuma kada Ka tozarta mu a ranar }iyama, Lalle ne Kai, ba Ka sa~awar alkawali.

Ya Allah! Ka kasa mini daga tsoron Ka abin da zaka shamakace tsakanina da sa~a maka, kuma daga ]a'arka abin da zaka isar dani aljannaka, kuma daga ya}ini abin da zaka sau}a}e mini da shi musiban duniya, kuma Ka jiyar dani da]i da jina da ganina da }arfina har abada, matu}ar Ka bar ni da rai, kuma kasa shi shine mai gado daga gareni, kuma kasa ramuwata a kan wanda ya zalunceni, kuma Ka bani nasara a kan wanda ya }iyayya da ni, kuma kada kasa musibata a cikin addinina, kuma kada kasa duniya itace babbar gurina, ko iyakar ilimina, ko zuwa wuta }arshena, kasa aljanna ita ce gidana, kuma kada Ka ]ora a kaina domin zunubaina wanda bai tsoronka ko yayi mini rahama, domin rahamarka, Ya Kai wanda yafi masu rahama rahama.

Ya Allah! Lalle ne ni ina neman tsari da izarka, ba abin bautawa da gaskiya sai Kai, daga Ka ~atar dani, Kaine rayayye wanda bai mutuwa, amma aljannu da mutane suna mutuwa.



Ya Allah! Ma}ir}irin sammai da }asa, Masanin gaibu da bayyane, ba abin bautawa da gaskiya sai Kai, ubangijin kome da mai mallakarsa, ina neman tsari da Kai daga sharrin shai]an da shirkinsa, da kuma in yiwa kaina abin da bayada kyau ko in jawowa wani Musulmi.

Ya Allah! Ka gyara mun addinina wanda yake shine abin kare al'amarina, kuma Ka gyara mini duniyata wadda take a cikinta ne rayuwata, kuma Ka gyara mini lahirata wadda take zuwa gareta ne makomata, kuma kasa rayuwa }aruwa ce gareni daga kowane alheri, kuma kasa mutuwa hutu ce gareni daga dukkan sharri.

Ya Allah! Lallene ina ro}onka lafiya a cikin duniya da lahira, Ya Allah! Lallene ina tambayanka afuwa da lafiya a cikin addinina da duniyata da iyalina da dukiyata, Ya Allah! Ka suturta alaurata, kuma Ka amintar da firgitata.

Ya Allah! Ka tsareni daga gabana da bayana da damana, da haguna, da samana, kuma ina neman tsari da girmanKa daga a cutar dani ta }ar}ashi na.

Ya Allah! Ka kyautata }arshena cikin al'amarina dukkan shi, kuma Ka bani ma}wabtaka (Ka tsirar dani) daga wula}ancin duniya da azabar lahira.



www.gph.gov.sa

Ya Allah! Ka taimakeni akan tunaka da gode maka da }yautata ibadarka.

Ya Allah! Lalle ne ina neman tsari da Kai daga gushewar ni'imarka, da juyawar lafiyarka, da ba zaton ramuwarka da kuma dukkan hushinka.

Ya Allah! Lalle Kai mai gafartawane, mai son gafartawa, saboda haka kayimun afawa. Ya Allah! Lalle ne ni ina tambayar Ka alheri dukkansa, na gaggawansa da na jinkirinsa, da wanda na sani daga gareshi da wanda ban sani ba, Kuma ina neman tsari da Kai daga dukkan sharri na gaggawansa da na jinkirinsa, da wanda na sani daga gareshi da wanda ban sani ba.

Ya Allah! Lalle ne ni ina tambayar Ka daga alherin da bawanka kuma annabinka Muhammad (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi) ya tambayeka. Kuma ina neman tsari da Kai daga sharrin da bawanka kuma annabinka muhammad (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gareshi) ya nemi tsari daga gareshi.

Ya Allah! Lalle ni ina tambayar Ka aljanna da abin da ke kusantarwa zuwa gareta na magana ko aiki, kuma ina neman tsari da Kai daga wuta da abin da ke kusantarwa zuwa gareta na magana ko aiki.



Ya Allah! Lalle ni ina tambayar Ka abubuwan da ke wajabta rahamarka, da han}urin samun gafararka, da ganima daga kowane aikin }warai, da tsira daga kowane zunubi, da samun nasara da aljanna, kuma da tsira daga wuta.

Ya Allah! Ka nisantar dani daga }yamammun halaye, da ayyuka da son zucciya da cututtuka.

Ya Allah! Ka gafartamun dukkan zunubaina kuma Ka shiryar dani zuwa ga halaye mafi kyau babu wanda zai iya shiryarwa zuwa ga mafi kyauwunansu sai Kai, kuma Ka kaudar dani daga miyagunsu babu mai kaudar da miyagunsu daga gare ni sai Kai.

Ya Allah! Lalle ni ina tambayar Ka tsoron Ka a ~oye da bayyane, kuma ina tambayar Ka kalmar gaskiya cikin hushi da yarda, kuma ina tambayar Ka daidaitua a cikin talauci da azziki, kuma ina tambayar Ka ni'ima wadda bata }arewa, da sanyin ido wanda bai yankewa, kuma ina tambayar Ka yarda bayan }ada'i, da sanyin rayuwa bayan mutuwa, da da]in kallo zuwa fuskar Ka mai karamci, da marmarin ha]uwa da Kai ba cikin wata cuta mai cutarwa, ko fitina mai ~atarwa. Ya Allah! Ka }awatani da kwalliya ta imani, kuma Ka sa mu shiryaryu masu neman shiryuwa ba ~atattu ba, kuma ba



www.gph.gov.sa

masu ~atarwa ba, masu zaman lafiya da masu ji~intar Ka, kuma maso ya}i da ma}iyan Ka, muna so da son Ka wanda yake son Ka, kuma muna }iyayya da }iyayya Ka wanda ya }iKa ko ya sa~a maKa.

Ya Allah! Ka cireni daga }as}ancin sa~o zuwa ]aukakar ]a'a, kuma Ka wadatar dani da halalin Ka daga haramin Ka, kuma da ]a'ar Ka daga sa~a maka, kuma da falalar Ka daga wanin Ka, Ya Rayayye, Mai tsayuwa da kome, Mai girman jalala da Karamci.

Ya Allah! Lalle ne ni ina neman tsari da Kai daga damuwa da ba}in ciki, kuma daga gazawa da kasala, kuma daga tsoro da rowa, kuma daga laifi da garama, kuma daga danniyar bashi da mazaje.

Ya Allah! Lalle ne ni ina neman tsari da Kai daga kuturta da hauka, da kuturta da mugunyar cututtuka.

Ya Allah! Ubangijin sammai da }asa, ubangijin al'arshi mai girma, Ubangijinmu da Ubangijin kome, mai tsagewar }wayar hatsi da kwalfar gurtsu, wanda ya saukar da attaura da injili da fur}ani, ina neman tsari da Kai daga sharrin dukka mai sharri wanda yake kana ri}e da gashin goshinsa.

Ya Allah! Kai ne na farko saboda haka babu wani abu



kafin Ka, kuma Kai ne na }arshe saboda haka babu wani abu bayan Ka, kuma Kai ne zahiri saboda haka babu wani abu a saman Ka, kuma Kai ne a ~oye, saboda haka babu wani abu a }asanKa, (ina ro}onKa) Ka biya mun bashi kuma Ka wadatar dani daga talauci.

Ya Allah! Kai ne Ubangiji na, ba abin bautawa da gaskiya sai Kai, Ka halittani kuma ni bawanKa ne, kuma in akan alkawalinka da wa'adin Ka gorgodon iyawata, ina neman tsari da Kai daga sharin da na aikata, na dawo maka da ni'imarKa akaina, nadawo maka da zunubi na, saboda haka kayi mini gafara domin babu wanda yake gafarta zunubai sai Kai.

Ya Allah! Lalle ne ina tambayar Ka (ikon) aikata ayyukan alheri da kuma barin muyagun ayyuka, da son miskinai, kuma Ka gafarta mini, kuma kayi mini rahama, kuma idan Kayi niyar fitinar bayinKa, Ka ]auki raina ba tare da Ka fitineni ba.

Ya Allah! Lalle ne ina neman tsari da Kai daga wahalar bala'i, da saduwa da Wahala, da mumunan }ada'i, da murnar ma}iya.

Ya Allah! Ya mai jirkita zukata! Ka tabbatar da zucciyata a kan addininKa, Ya Allah! Ya mai juya zukata da Idanu, Ka juya zucciyata a kan ]a'arKa.

Ya Allah! Ka da Ka barni da wani zunubi face Ka gafarta mun shi, ko kuma wani damuwa face Ka sau}a}e shi, ko wani bashi face Ka biya shi, ko wata bu}ata daga cikin hajojin duniya da lahira wadda take a gare Ka abun yarda kuma muna da gyaruwa a cikinta face Ka biya muna bu}atar, Ya wanda yafi yin rahama a cikin masu yin rahama.

Ya Ubangijinmu! Ka kar~a daga garemu, lalle ne Kai mai jine masani. Kuma da yafe muna, lalle ne Kai mai yawan yafewane mai jin}ai.

Ya Ubangijinmu! Ka yi gafara a garemu, kuma ga 'yan 'uwanmu, wa]anda suka riga mu yin imani, kada Ka sanya wani }ulli a cikin zukatanmu ga wa]anda suka yi imani. Ya Ubangijinmu! Lalle Kai ne Mai tausayi, Mai jin }ai.

Ya Allah! Lalle ni bawanKa ne ]an bawanKa ]an baiwarKa, gashin goshina yana hannunKa, hukunciKa akaina mai zartarwane, Kuma }ada'inKa a kaina adalcine, ina ro}onka da kowane suna wanda yake naKa ne Kasa ma kanKa ko Ka saukar dashi a cikin littafinKa ko Ka sanar da shi wani daga cikin halittarKa, ko Ka ka]aita da shi cikin ilmin gaibu a wurinKa, da Ka saka al}ur'ani mai girma rabi'in zucciyata da hasken }irjina,



da jaye ba}in cikina da barin damuwata.

Ya Allah! Ka sanar da ni daga gareshi abunda na jahilceshi, kuma Ka tunatar dani daga gareshi abunda na manta, kuma Ka azurtani da karantashi cikin dare da rana a bisa fuskar da zata yardar da Kai ni, da rahamar Ka, Ya wanda yafi yin rahama a cikin masu yin rahama.

Ya Allah! ! Lalle ne ina neman tsari da Kai daga azabar jahannama, da azabar }abari, kuma ina neman tsari da Kai daga fitinar masihid dajjal, kuma ina neman tsari da Kai daga fitinar rayuwa da Mutuwa. Ya Allah! ! Lalle ne ina neman tsari da Kai daga laifi da garama.

Ya Allah! Ka gafarta mun, kuma Ka shiryar dani, kuma Ka azurtani, kuma Ka warkar dani, kuma kayi mini rahama. Ya Allah! Lalle ne ina tambayarKa mafi alherin abin tambaya, da mafi alherin addu'a, da mafi alherin cikin nasara, da mafi alherin aiki, da mafi alherin sakamako, da mafi alherin rayuwa, da mafi alherin mutuwa, kuma Ka tabbatar dani, kuma kasa mizanina yayi nauyi, kuma Ka tabbatar da imanina, kuma Ka ]aga darajata, kuma Ka kar~i sallata, kuma Ka yafe kurakuraina, kuma ina tambayarKa darajoji masu ]aukaka daga aljanna. Ameen.

Ya Allah! ! Lalle ne ina ro}onka mabu]an alheri da

}arewa da Alheri, da farkonsa, da }arshensa, da zahirinsa da ba]ininsa, da darajoji masu ]aukaka daga aljanna. Ameen.

Ya Allah! ! Lalle ne ina ro}onka Ka ]aukaka ambatona, kuma Ka yafe laifina, kuma Ka gyara al'amarina, kuma Ka tsarkake zucciyata, kuma Ka tsare farjina, kuma Ka haskaka zucciyata, kuma Ka gafarta mun zunubina, kuma ro}onka darajoji masu ]aukaka daga aljanna. Ameen.

Ya Allah! Lalle ne ina ro}onka Ka da Ka yimini albarka a cikin raina da a cikin jina, da ganina, da a cikin ruhina, da a cikin halittata, da a cikin halayena, da a cikin iyalina, da a cikin rayuwata, da a cikin mutuwata, da a cikin aikina, kuma Ka kar~i ayyukan alherina, kuma ro}onka darajoji masu ]aukaka daga aljanna. Ameen.

Ya Allah! Ka tsareni da Musulumci a tsaye, Ka tsareni da Musulumci a zaune, Ka tsareni da Musulumci a kwance, kuma kada Ka darantar da ma}iyi game da ni, ko mai hasada.

Ya Allah! Ka nisantar tsakanin ni da kurakuraina kamar yadda Ka nisantar da yamma da gabas. Ya Allah! Ka tsabtacemu daga kurakuranmu kamar yadda a ke tsabtace farin tufa daga datti. Ya Allah! Ka wankeni



daga kurakurai da }an}ara, da ruwa, da sanyi.

Ya Allah! Kai ne Sarki, ba abin bautawa da gaskiya sai Kai, Kai ne Ubangijinmu, kuma ni bawanKa ne, na zalunci kaina, kuma ina i}irari da zunubina, saboda haka Ka yafe mun dukkan zunubaina, domin babu wanda yake gafarta zunubai sai Kai, kuma Ka shiryar dani zuwa ga mafi kyawawan halaye, babu mai shiryarwa zuwa ga mafi kyawawansa sai Kai, kuma Ka kaudar dani daga miyagunsu babu mai kaudarwa daga gareni miyagunsu sai Kai, Ina me ansa kiranKa da faranta maKa rai, Alheri dukkansa yana hannunka, kuma sharri bai kasance zuwa gareka ba, Ni da Kai ne kuma zuwa gareKa, Ka tsarkaka kuma Ka ]aukaka, ina neman gafara kuma ina tuba zuwa gareka.

Ya Allah! ! Lalle ne ina neman tsari da Kai daga a mayar dani zuwa mafi }as}ancin rayuwa, kuma ina neman tsari da Kai daga bushewar zucciya da gafala, da wul}anci da talauci, kuma ina neman tsari da Kai daga kafirci.

Ya Allah! ! Lalle ne ina neman tsari da Kai daga sharrin da na aikata da kuma sharrin da ban aikata ba, Kuma ina neman tsari da Kai daga sharrin da na sani da kuma sharrin da ban sani ba.



www.gph.gov.sa

Ya Allah! ! Lalle ne ina neman tsari da Kai daga rushewar gida, da fa]owa, kuma daga nutsewa ruwa da }una, da tsufa, kuma ina neman tsari da Kai daga shai]an kada ya ru]ani lokacin Mutuwa, Kuma ina neman tsari da Kai daga in mutu ta hanyar }ari, kuma ina neman tsari da Kai daga kwa]ayin da ke kaiga aibi.

Ya Allah! Lalle ne ina ro}onKa tabbatarwa a cikin al'amarin da dogewa a kan shiryuwa, kuma ina tambayar Ka godiyar inimarka, da kyautata ibadarKa, kuma ina ro}onKa zucciya lafiyayya, da harshe mai gaskiya, kuma in ro}onka daga alherin da kasani, kuma ina neman tsari da Kai daga sharrin da Ka sani, kuma ina neman gafara daga abin da Ka sani, kuma lalle kai ne masanin gaibu.

Ya Allah!Kayimin ilhamin shiryuwata, kuma Ka kareni daga sharrin raina, Ya rawayye, Ya tsayayye a kan kome, Ya Allah! Ka }arani kuma kada Ka rage ni, kuma Kayi mun karamci kuma kada Ka wula}antani, kuma Ka bani kada Ka hana ni, kuma Ka za~eni akan wa]ansu amma kada Ka barni ba za~a~~eba, Ya mai girman jalala mai karamci.

Ya Allah! Ina ro}onka rahama daga gareka Ka na mai shiryar da zucciya ta da ita, kuma Ka ha]a al'amarina da ita kuma Ka tara abinda ya wargaje na al'amarina da ita,



kuma Ka tsare abinda ya ~oyu na al'amarina da ita, kuma Ka ]aga abinda ya bayyana na al'amarina da ita, kuma Ka mai da fuskata fara da ita, kuma Ka tsarkake aiki na da ita, kuma kayi mini ilhamin shiryarwa da ita, kuma Ka mayar da fitinai daga gareni da ita, kuma Ka tsareni daga dukkan mugun abu da ita.

Ya Allah! Ina ro}onka lafiya a cikin (halin) imani, da imani cikin hali mai kyau, da tsira wadda nasara ya ke bi, da rahama daga gareka, da lafiya daga gareka, da gafara da yarda.

Ya Allah! Lalle ne Ka na jin maganata kuma Ka na ganin wurina, kuma Ka san sirrina da bayyane na, kuma babu abinda ya ke a ~oye na al'amarina a kan Ka, Kuma ni fa}iri ne mai iyakar talauci, mai neman taimako, da ma}wabtaka, da tsoro, da tausayi, da tabbatarwa da i}irari gare Ka ga laifinsa, ina ro}onka, ro}on miskinai, kuma ina }an}antar da kai zuwa gare Ka irin }an}antar da kan mai zunubi }as}antacce, Ina ro}onka da irin addu'ar mai tsoro makaho, addu'ar wanda wuyansa ya ya mi}a maka, kuma jikinsa ya wula}antar domin kai, kuma hancinsa yasa a cikin kasa domin Ka, saboda haka, Ya Allah! Ka kar~i tuba ta, kuma Ka wanke laifi na, kuma Ka ansa addu'ata, kuma Ka tabbatar da hujjata, kuma Ka shiryar da zucciyata, kuma Ka daideta halshe na, kuma Ka zare }iyayya daga zucciyata, Ya



www.gph.gov.sa

mafi rahamar masurahama.

Ba abin bautawa da gaskiya sai Kai, tsarki ya tabbata a gare Ka, lalle ne na kasance daga cikin azzalumai.

Ubangijinmu! A kan Ka muka dogara kuma zuwa wurin Ka muka dawo, kuma zuwa gare Ka makomarmu take. Ubangijinmu! Kada Ka samu fitina ga wa]anda suka kafirta, kuma Ka gafarta muna, Ubangijinmu! Lalle ne Kai mabuwayi ne, Mai hikima.

Tsarki ya tabbata ga UbangijinKa, Ubangijin rinjaye, daga barin abin da suke siffantawa. Kuma aminci ya tabbata ga Manzanni. Kuma godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin halittu.

www.gph.gov.sa



## Abubuwan Da littafin ya }unsa.


Gabatarwa ........ 3
Bayanin farko na littafin ........ 5
Falalal Hajji da Umra ........ 7
Mi}atai ........ 9
Ire'iren Ayyukan Hajji ........ 13
Rukunnan Hajji ........ 15
Wajiban Hajji ........ 15
Rukunnan Umra ........ 16
Wajiban Umra ........ 16
Abubuwan Da Aka Hana Yinsu A Cikin Halin Ihrami ........ 17
Hukuncin wanda ya aikata wani abu daga cikin wa]annan abubuwan da aka hana ........ 19
Mi}idarin Fidiya ........ 20
Sifar Ihrami domin yin Umra Da Hajji ........ 23
Sifar Ihrami ........ 23
Sifar Umra ........ 26
Sifar Hajji ........ 31
Shiryarwa ga Alhazai da masu umra ........ 36
Fa]akarwa akan wa]ansu kurakurai ........ 43
Na Farko: Kurakure Game Da Ihrami ........ 45
Na Biyu: Kurakure Game Da [awafi ........ 47
Na Uku: Kurakure Game Da Sa'ayi. ........ 49
Na Hu]u: Kurakure Game Da Arafa. ........ 51

Na Biyar: Kurakure Game Da Muzdalifa.........52
Na Shida: Kurakure Game Da Jifa. ....................53
Na Bakwai: Kurakure Game Da Muna. ............56
Na Takwas: Kurakure Game Da Fita Daga Masallacin Haram. ..........................................57
Shiryarwa Ga mai ziyarar Masallacin Manzo.........58
ZA|A||UN ADDU'OI...............................................63

**_Al-Barakati Printers_**

***Makkah – Tel. : 5451677 – Fax : 5451678***

الرئاسة العامة لشؤون المسجد الحرام والمسجد النبوي
www.gph.gov.sa